

Yantuwa daga Kunya

Yesu ya ɗauki kunyar mu domin mu sami ɗaukakar Sa



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Kunya wani irin yanayi ne mai muni da damuwa, ana kuma samun ta har a cikin Krista. Sau da yawa sakamako ne na cin zarafi ta wurin jima'i ko cin zarafi, kamar dai yi wa mutum ba'a a makaranta. Na taɓa karanta labarin wani shugaban makaranta wanda ya nuna wani yaro ya ce masa ya tashi tsaye, sannan ya ce wa dukan ajin, "Dukan ku kun ci jarrabawarku banda shi kadai." Me wannan saurayi zai ji in ban da kunya? Yawancin ɗanɗanon da suka faru a lokacin ƙuruciya na iya haifar da kunya. Waɗanda suka faru tun da daɗewa a wani lokacin yana da wahala a kawar dasu. Abin da ya faru a farko galibi yakan zama har ƙarshe.

Watakila abin da ya fi bada kunya a cikin wayewarmu na ƙasashen Turai shi ne cin zarafi ta wurin jima'i (har ga masu kiran kansu Krista). Na yi gwagwarnaya da waɗanda suka shiga cikin irin wannan matsalar da yawa. Sai dai idan sun zo wurin gicciye ne kaɗai za su sami 'yantarwa daga wannan kunyar. Wannan furucin annabci ne da ya bayyana abin da Yesu ya yi mana:

> "Ubangiji Yahweh ya buɗe kunnena; [Yesu] ban yi tayarwa ba, ban kwa bada baya ba. Na bada bayana ga masu bugu, kumatuna kuma na bayar ga masu tuge gashi, ban ɓoye fuskata daga kunya da zubda miyau ba." (Ishaya 50:5–6)

Yesu ya ce, "Na bada bayana ."Zai iya ceton kan Sa; zai iya kiran rundunan mala'iku goma sha biyu domin su cece shi (dubi Matta 26:53). Amma bai yi ba. Ya bada bayan Sa. Hotunan da muke gani na bulalar Yesu ne wanda ba iri ɗaya suke da abin da muka sani a zahiri ba. Wannan mummunan yanayi ne domin bulalar tana da guntayen ƙarafa ko ƙasusuwa a cikin harsunanta. Lokacin da suka taba jikin mutum, suna cire fatar su fitar da naman jikin. Wannan shi ne abin da Yesu ya daure domin mu. Kuma bai ɓoye fuskarsa ga jin kunya da tofa yawu ba. A kan giciye, Yesu ya ɗauki kunyarmu.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa a kan gicciye, Yesu ya 'yantar da ni daga kunya—domin ya ɗauki kunyata don in sami ɗaukakar Sa. Amin.


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-134-HAU

Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.